SASHI NA 3

**ABUBUWAN MASU YAWA MA BANBANTA A GAREMU**

# Mataki na gab

Bayanai da katunan halaye: Yankin Sahel Africa




THE LOCAL
CHANGEMAKERS
COURSE

# Bayanai da katunan halaye: Yankin-Sahel Africa

A cikin wannan takarda, za ku iya samun katunan halaye da bayanan da za ku iya gyarawa, bugawa, da amfani da su lokacin da kuke gudanar da aikin 'Mataki na gab' (wanda aka samu a Sashi na 3 na Koyarwar Masu kawo Sauyi na Asali). An ts ara waɗannan katunan da bayanan don ƙasashen da ke cikin yankin Sahel – ƙasashen da galibi suna da rinjayen Kirista da Musulmi a sassa da ban-daban na ƙasar (ko ƙananan rinjaye). Yi amfani da jagorar da keƙasa don zabar waɗanne halaye da bayanan da za ku yi amfani da su kuma ku daidaita su da yanayin rukunin ku.

## Bayanai

### Jagora domin zabar bayanai

Kuna buƙatar bayanan 12 - 15. An samar da jerin bayanan kusan 30 don zaɓar daga ciki.
An gabatar da bayanan a cikin rukunoni biyar masu zuwa:

- Girmamawar jama'a da ƙarfin gwiwa.
- Karfin yin zaɓi.
- Jin daɗin rayuwa da tsaro.
- Rauni ga nuna bambanci ko tashin hankali.
- 'Yancin Yin Addini da Yin Aiki da Shi.

Zaɓi aƙalla bayanai 2 daga kowane rukuni, bisa ga yanayin da kuke tsammanin ya fi dacewa da yanayin ku. Gyara bayanan idan ya cancanta.

| GIRMAMAWAR JAMA' A DA KARFIN GWIWA |
|---|
| Ana girmama yarenku, addininku, da al'adunku a cikin jama' arku. |
| Kuna jin ra'ayoyinku suna da mahimmanci kuma ana sauraron ra'ayoyinku kuma ana neman su daga waɗanda ke kewaye da ku. |
| Kuna jin daɗin yin magana a bainar jama'a da bayyana ra'ayoyinku. |
| Kuna jin cewa ƙwarewarku tana da godiya kuma ana girmama ta daga waɗanda ke kusa da ku da kuma jama'ar gaba ɗaya. |
| **KARFIN ZUCIYAR YI ZABI** |
| Kuna shiga cikin yanke shawara ga me da manyan sayayya don gidanku. |
| Kuna iya saduwa da abokai kuma ku yi tafi ye- tafi ye don saduwa da dangi ba tare da neman izinin kowa ba. |
| Kuna iya zuwa makaranta, yin karatu, da yin aikin da kuka zaɓa. |
| Kuna iya soyayya da wanda kuka zaɓa, koda kuwa suna da addini daban da ku. |
| Kuna iya samun saki idan kuna buqata, ba tare da tsoron hukunci daga waɗanda ke kewaye da kuba (misali ta hanyar keɓancewa daga hanyoyin sadarwar zamantakewa). |
| Kuna iya zaɓe a zaɓen ƙasa da na gida. |
| Kuna iya samun duk wani abin sha'awa, yin duk wasu wasanni, ko kallon duk wasu fina finai da kuke so. |
| Kuna iya yanke shawara game da jikinku - misali yawan yaran da za ku haifa da lokacin da za ku haifa. |

| JIN DAƊIN RAYUWA DA TSARO |
|---|
| Ku da danginku ba ku da rauni ga bala'o'i na yanayi. |
| Kuna da isasshen damar samun kulawar likita da fa' idodin zamantakewa/ragama na tsaro idan kuna rashin lafiya ko rashin aikin yi. |
| Kuna iya ba wa yaranku abin da suke buƙata don girma cikin ƙoshin lafiya kuma ba ku jin tsoron makomarsu. |
| Kun son abin da za ku yi da inda za ku nemi taimako idan kun shiga cikin wahala. |
| Kuna jin za ku iya ci gaba a cikin aikinku kamar yadda kuke so. |
| Kuna da damar samun bayanai da yawa game da ciwon ƙwayar SIDA da sauran cututtukan da ake ɗauka ta hanyar jima'i. |
| **RAUNI GA NUNA BAMBANCI KO TASHIN HANKALI** |
| Ba ku taɓa jin an nuna muku bambanci ba saboda ƙabilarku, matsayinku, ko addininku. |
| Ba ku jin tsoron tsayar da 'yan sanda kuma ba a taɓa kama ku ba. |
| Kuna samun tsaro a gida da kan titi kuma ba ku damu da cin zarafi ba, cin zarafi na jima' i, ko cin zarafi na kan titi ba. |
| Littattafan makaranta sun ba ku ra'ayi cewa mutane kamar ku mutane ne masu kyau a cikin jama'a waɗanda za su iya cimma komai. |
| Ana nuna addininku, ƙabilarku, ko wani asalin ku a cikin kafofin watsa labarai. |
| Ba ku da matsala wajen samun sabon katin shaida, kuma amfani da katin shaidar ku baya haifar da nuna bambanci. |
| **YANCIN SAMUN ADDINI DA YIN AIKI DASHI** |
| Kuna iya yin bikin manyan bukukuwan addini, duka tare da mutanen da ke kusa da ku da kuma a bainar jama'a. |
| Kuna iya yin tafiya zuwa ƙasashen waje don aikin hajji, ziyara, don saduwa da masu imani tare, ko don halartar taron ƙasa daaƙsa. |
| Kuna iya yin addu'a a bainar jama'a kuma ku halarci wurin ibadar ku a ko da yaushe. |
| Kungiyar addinin da kuke ciki za ta iya gina ko buɗe wurin ibada ba tare da fuskantar matsaloli daga hukumomi ko wasu ƙungiyoyi a cikin jama'a ba. |
| Kuna iya kasancewa a buɗe tare da ra'ayin duniyar ku ga dangi, abokai, da abokan aiki kuma ku yi magana game da shi a kafofin watsa labaru ba tare da tsoron sakamako ba. |
| Kuna iya samun, karantawa, da raba bayanai ga me da addininku ko i maninku cikin yardar rai. |
| Ba za ku rasa abokanku ko matsayin zamantakewa ba idan kun koma wani addini daban. |

# Katunan halaye

## Jagora don zaba da daidaita halaye

Kuna buƙatar hali 1 ga kowane mahalarci. An gabatar da halayen da aka gabatar a shafukan da ke gaba a cikin rukunoni 5:

- Halaye masu iko na zamantakewa, siyasa, ko addini da/ko yan raunuka.
- Halaye masu rauni da suka shafi haɗakar addini/imani da jinsi.
- Halaye masu rauni da suka shafi asalin addini ko imani.
- Halaye masu rauni da suka shafi matsayi, aji, matsayin baƙi, ko wasu dalilai.
- Wasu halaye.

#### KARA KO RAGE HALAYE

Yi tunani game da jerin halayen da aka bayar:

- Shin akwai wasu halaye da basu da alaƙa da yanayin ku-share waɗannan ko gyara su don su dace.
- Shin akwai wasu halaye masu mahimmanci ga yanayin ku da suka ɓace, misali mutum daga wata ƙungiyar addini, ƙabila, ko zamantakewa? Kara waɗannan, kiyaye bayanin halin a takaice. (**Ain Lura**: Kada ku ƙara da yawa! Sai dai idan kuna da babban rukuni, dole ne ku yanke halaye don dacewa da giman ƙungiyar ku.)

#### ZAƁI HALAYE

- Tabbatar kun haɗa da halaye daga kowane rukuni.
- Ba fiye da ɗaya cikin shida halayen da aka zaɓa ya kamata ya fito daga rukunin da ke da iko ba.
- Zaɓi yawan/waɗanne halaye za ku zaɓa daga wasu rukunoni bisa ga waɗanne raunuka suka fi dacewa kuma suna da mahimmanci don haskakawa a cikin yanayin ku.
- Haɗa da kewayen asalin addini/imani da daidaiton halayen maza da mata.

#### GYARA HALAYE IDAN ANA SO

Mahalarta za su iya shiga tare da halayen sosai idan kun ɗan ɗauki lokaci don sanya halayen cikin yanayin ƙasar ku. Misali, kuna iya gyara halayen don tantance wurin da halin ke zama, su na hukumar jihar da suke aiki a ciki, da sauransu. Wannan ba shi da mahimmanci don aikin ya yi aiki.

## BANGARE

Halaye masu iko na zamantakewa, siyasa, ko addini da/ko yan raunuka.

**An san ka, ana girmama ka kuma kai jagora ne mai iko a tsakanin mafiya yawan al'umma masu addinai.**

**Ke mace ce daga yammacin duniya da kike aiki wa ƙungiya da ba ta gwamnati ba a babban birni.**

**Kina karantar wa a karamar makarantar Islamiyya a wani ƙaramin garin da musulmai ke da rinjaye.**

**Kai mutum ne mai takawa, dake aji matsakaici daga al'umma masu addini da rinjaye.**

**Kai ɗan majalisa ne dake wakiltan jam'iyya a gwamnatin yanzu.**

**Kai babban hafsan soja ne.**

## BANGARE

Halaye masu rauni da suka shafi haɗakan addini/imani da jinsi.

**Ke mace musulma ce wacce so da dama ta sha duka a hannun mijin ta.**

**Ke mace Kirista ce wacce so da dama ta sha duka a hannun mijin ta.**

Ke yar shekara 16 ce musulma.
Iyayen ki sun kasance talakawa ne,
kuma suna zaune a ƙaramin gari.
Kina so ki shiga jami'a kuma
baki son ayi miki aure a ƙananan shekaru.

Ke karamar yarinya ce dake da zama a qauye.
Ba kya so ayi miki kaciya ko ki yi aure
a ƙananan shekaru amma kuma haka
ake sa rai a cikin al'umma.

Ke uwa ce da baki da miji
kina zaune cikin al'ummar
kirista masu tsantseni.

Kai ɗan kirista ne dake son yar musulmai.
Duka iyayen ku biyu zasu ki
soyayyar idan suka sani.

Ke kirista ce yar madugo kuma kina
zaune da abokiyar harkar ki.
Kina so kifito ki je ga iyalan ki.

## BANGARE

Halaye masu rauni da suka shafi
asalin addini ko imani.

Ke 'ya mace ce musulma da ta koma cikin
kiristoci masu rinjaye domin neman aiki.
Kayan ki sun sanya ki fita daban kuma
hakan yasa kike jin ana raina ki.

Ke mace ce kirista da ta koma cikin
musulmai masu rinjaye domin aiki.
Kayan ki da tsarin gashin ki yasa kin fita da ban.
Ana hantarar kiristotin da suka shigo.

Kai matashin musulmi ne dake da gashin gemu
kuma kake da zama ayankin da kiristoci ke da
rinjaye. Kwanannan ƙungiyar ta'addanci dake
da alaƙa da musulunci a ƙasar suka kai mishi hari.

Kai fasto ne kuma kirista wanda ke aiki da
ƙungiyar mabiya addini ƙarama a yankin ƙasar
dake da musulmai masu rinjaye.

Ke matashiyar yarinya ce da ta sauya daga musulunci zuwa kiristanci. Iyalan ki ba su san cewa kin chanja addinin ki ba har yanzu.

Ke mace ce mai matsakaicin shekaru dake yin addinin gargajiya. Kin ƙi amincewa da musulunci da kiristanci.

Ke ‘yar shekaru 16 ce musulma dake zaune a sansanin ‘yan gudun hijira saboda tarzomar ‘yan ƙungiyoyin ‘yanjihadi. Iyayen ki suna damuwa da tsaron ki da mutunci ki kuma suna duba yiwuwar auren ki.

Kai matasahin yaro kirista ne dake zuwa makarantar kwana a qauyen. Wasu yara daga maqwabtan gunduma a ƙungiyar ‘yanta’adda dake da alaƙa da musulunci sunyi garkuwa dasu.

Baka da addini. Ka shiga gangamin kawo ƙarshen amfani da addini a siyasa da dokoki. An san fafutukar da ka ke yi, kuma ana ganin hakan da kake yi ba dabi‘ar yan Afrika bace.

## BANGARE

Halaye masu rauni da suka shafi matsayi, aji, matsayin baƙi, ko wasu dalilai.

Kai namiji ne dake aikin da ake biyan ka kudin ƙwadago kullum. Ka na zaune ne a gurbataccen yanki dake kusa da babban birni. Kana ƙoƙarin ka mallaki lasisin tuƙi don ka zama direban ƙaramar Bas.

Kai dattijo ne mai fama da nakasa a ƙauye. Dan ka zai koma babban birni da iyalan shi.

Ke da mijin ki manoma ne kiristoci kuma Makiyaya masu yawo wasu lokuta na wuce wa ta gonar ku tare da lalata muku amfanin gona. Makiyaya masu dauke da makamai wasu lokutan sun kai hari kan wasu gonaki. Tunanin ka shine gonakin kiristoci ne musamman suke da hadarin fuskantar hari.

Ke mace ce daga al‘ummar makiyaya masu yawo. Chanjin yanayin amfani filaye da dumaman yanayi yana saka muku rayuwa cikin ƙunci. Ke musulma ce kuma kina yin addinin gargagjiya.

Ke mace ce dake da ƙaramar gona. Filin noman ki baya samar da amfanin gona isasshe don ciyar da iyalan ki kuma gonar na ƙara fuskantar zaizayewar ƙasa a sanadiyyar dumamar yanayi.

Ke macen da mijin ki ya rasu ya bar ki da yara uku. Kowa ya san cewa mijin ki ya mutu ne saboda cutar sida (AIDS) kuma daya daga cikin yaran ki yana da dauke da cutar ta sida wato AIDS.

BANGARE

Wasu halayen.

Ke mace ce daga ƙauyen dake da alaƙa da shiga ƙungiyar ta'addanci kuma tana ayyukan ta a wasu sassan ƙasar.

Kai memba ne a ƙungiyar samar da zaman lafiya da aka tura a ƙasar ƙarƙashin Majalisar Dinkin duniya/ECOWAS/CEDYAO.

(Kara wasu halayyan a nan.)

(Kara wasu halayyan a nan.)

(Kara wasu halayyan a nan.)

(Kara wasu halayyan a nan.)

(Kara wasu halayyan a nan.)